# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da

# Yona da babban kifi



**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Jonathan Hay**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Mary-Anne S.**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan**
**har ba zaku sayar da shi.**

**Shekarun baya da dama, an yi wani mutum mai suna Yona a kasar Isra'ila. Wata rana Allah ya gaya masa ya tafi Nineba, birni mafi girma da iko a dukan duniya a lokacin.**



**Yona zai je garin don ya ja mutanen kunne cewa Allah yana sane da muguntansu.**



**Yona ya yi wa Allah rashin biyayya! Maimako ya je Nineba, Yona ya shiga jirgin ruwa ya kama hanya zuwa wani wuri dabam zuwa gari mai suna Tarshish.**



**Ubangiji Allah ya aiko da babbam iska a tekun. Sai aka yi babban hadari! Masu tukan jirgin suka ji tsoro watakila jirgin ruwan zai kakkarye ya lume cikin tekun.**



**Hadarin ya yi ta karuwa. Cikin tsoro mai tsanani, masu jirgin suka yi addu'a ga allolinsu suka ciccire kaya suna jefar wa a tekun domin su rage nauyin kaya a cikin jirgin. Amma yin haka bai taimaka ba.**



**Yona ne kadai a cikin jirgin wanda ba ya addu'a. Maimmaiko, yana kwanciye a cikin jirgin, yana barci mai zurfi. Shugaban masu tukan jirgin ya same shi. "Mene ne kake yi kana barci? Tashi! Ka yi addu'a ga Allahnla! Watakila Allah zai tuna da mu, don kada mu halaka."**



Sai suka gane cewa damuwansu yana da dangantaka da Yona. Sai ya gaya musu cewa yana gudu ne daga wurin UBANGIJI. Sai suka tambaya, “Mene ne za mu yi da kai, domin tekun ya kwanta domin mu?” “Ku dauke ni sama sai ku jefa ni a cikin tekun,” Yona ya amsa. “Gama na tabbata saboda ni ne wannan babban hadarin ya zo muku.”



Masu jirgin ruwan ba su so su jefar da Yona a cikin tekun ba.  Sai suka yi kokari su kai jirgin a bakin teku.  Amma ba su iya ba.  Akwai wani abu daya tak wanda za su yi!



**Bayan yin addu’an neman yafewa, sai masu tukan jirgin suka daga Yona sama suka jefar da shi a gefen dayan. Yayinda Yona yana lumewa a cikin ruwan, sai tekun ya kwanta tsit sai isakar ta daina.**



**Yadda yanayin ya canja nan da nan ya ba wa masu tukin jirgin tsoro fiye da hadarin da suka fuskanta. Babu shakka, sun gane cewa Allah ne kadai wanda zai iya aikata wannan. Cikin tsoro da mamaki, sai suka yi wa Allah sujada.**



Amma dai, wannan dan aika marar biyayya ya sami abin ba da mamaki.  Cikin lumewa a cikin ruwan babu taimako, Yona ya sani cewa babu abin da zai iya cece shi daga mutuwa na ruwa.
Da ya sha ruwa har mutuwa, kuma – amma Allah yana da shiri dabam.



**UBANGIJI ya shirya wani babban kifidon ya hadiye Yona. Kifin ya zo daidai lokaci! Kurbawa sau daya kawai, Yona ya bar teku zuwa ciki cikin kifi. Yona ya zauna a ciki cikin kifi na kwana uku. Ya sami isashen lokacin tunani da addu’a.**



**Bayan kwana uku, Yona akarshe ya yi alkawari zai yi biyayya ga Allah.  Nan take, Allah ya yi magana da kifin, sai ya yi aman Yona a bakin tekun.**



**Sau daya kuma, Allah ya gaya wa Yona ya tafi Nineba ya yi wa’azin kalmar Allah. Wannan karon, Yona ya tafi! Yona ya shiga birnin, yana ihu, “A kwana arba’in, za a ci nasara kan Nineba.”**



**Mutanen Nineba suka ba da gaskiya ga kalmar Allah. Suka yi azumi, suka rufe rigunan nunan bakin ciki don su nuna cewa sun tuba daga zunubansu. Ko sarki ma ya kaskantar da kansa a gaban Allah. Ya auka daga kursiyinsa, ya saka rigunan nunan bakin ciki, ya zauna a cikin toka. Ya ba da umurni kowa ya tuba daga mugaye halinsa da mugunta, sai kowa ya yi addu'a don UBANGIJI ya yafe su.**



Allah kuwa ya yafe su! Lallai rana farin ciki mai yawa ne a birnin Nineba sa’ad da mutanen suka gane cewa Allah ya riga ya yafe musu zunubansu. …Amma mutum daya ya kasance da bakin ciki mai yawa. Yona!





Don me Yona ya yi fushi? Ya ce wa Allah, “Na sani cewa kai Allah mai alheri da jinkai ne, mai jinkirin fushi, mai yawan kirki.” Wato, Yona ya sani cewa kullum Allah yana yafe wa wadanda suka tuba daga zunubansu suka kuma yi biyayya ga Kalmar Allah. Ya nuna kamar Yona bai so mutanen Nineba ba.  Bai so a yafe musu zunubansu ba.

**Yona ya yi fushi da Allah sosai har ya ce, "Dauki raina daga gareni; gama mutuwa ta fi mini kyau fiye da rai."**



Yona ya zauna a bayan garin, yana jira ya ga abin da Allah zai yi nan gaba.  Ubangiji Allah ya shirya wani itace mai manyan ganye.  Ya yi girma da sauri-sauri, Yona ya zauna a inuwarsa daga zafin rana duka yini.



**Washegari, Allah ya aika da kwari, wanda ya cinye itacen. Sa'an nan Ubangiji ya shirya isak mai zafi mai karfi wanda ya jiji wa Yona har yana gani kamar zai mutu. Duka wannan ya kara ba wa Yona fushi.**



Sai Ubangiji ya ce wa Yona, “Ko kana da ‘yanci ka yi fushi?  Ka tausaya wa itacen inabin da ba ka yi aiki a kansa ko ka sa ya yi girma ba.  Ta bullo da daddare sai ta bushe da daddare.



Don me ba zan yi jinkai a kan
Nineba, wannan babban birni, da
dubun-dubban mutanenta ba?”



# Yona da babban kifi

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**Yona**

**“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130**

# KARSHE



60

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**